# KWARI MASU CUTA MA WAKE DA MASU TAIMAKA MISHI

I., Baoua[1], D., Burruss[2], M., McClellan[2], L., Karimou[1], L., Amadou[1], L., Massaoudou[3] G., [4]Pittendrigh, B.R.

[1]Institut National de la Recherche Agronomique du Niger, BP 429 Niamey Tél: +227 20 72 27 80 Email, : inran@intnet.ne ou dginran@yahoo.com; [2]Peace corps, B.P. 10537. Niamey, Niger
[3] Direction Régionale de l'Alphabétisation de Maradi, Tél: 96897035 Email: massaoudougarba@yahoo.fr [4]Department of Entomology, University of Illinois at Urbana Champaign, IL, USA

Dry Grain Pulses CRSP

## Kaskar Gindin Wake



**Hausa** – Ɗan Maski ko Darɓa
**Français** - Les Pucerons
**Scientifique** - *Aphis craccivora*

Ɗan Maski ko Darɓa yana rayuwa kwana 6 zuwa kwana 15 kuma yana aihuwa kimanin ɗiya 100. Darɓa tana kasar tohon wake kuma ana samunta cikin tushe da huren wake. Wake yana iya samu matsala daban- daban saboda Darɓa, amma akwai wani irin wake wanda ke jimre ma Darɓa. Ruwan sama yana rage Darɓa in ana yinsu kai a kai kuma ana iya aiki da maganin gargajiya ko na zamani.



**Hausa** - ƙananan darɓa
**Français** – jeunes pucerons
**Scientifique** - *Aphis craccivora*

## Kaskar Huren Wake



**Hausa - Bunsuru**
**Français** - Thrips
**Scientifique** - *Megalurothrips sjostedti*

Bunsuru yana rayuwa kwana 14 zuwa kwana 18, yana sakin ƙwai shin ciki hure. Bayan sun girma za su ɓata huren. Ana iya kashe shi da maganin zamani ko na gargajiya.



**Hausa - hangara**
**Français** - Mylabres
**Scientifique** - *Mylabris senegalensis*

Hangara ita ma tana cin huren wake. A yi hankali in kun shibka wake kusa da massara. Hangara za ta yi ɓarna diwa bisa waken saboda tana zuwa bisa huran massarar . To huren wake yana hitarwa galibi rana guda akwai wuya in kashe Hangara da maganin kashe ƙwarin wake.

## Kwari masu taimaka ma wake



Mai ɗashi bakwai ja tana ɗaya daga cikin kankanan ƙwarin da ke taimaka ma wake saboda yana cin Darɓa.

**Hausa**- Mai ɗashi bakwai ja
**Français** - Coccinelle
**Scientifique** – *Cheilomenes sulphurea*



Akwai mai shayi ukku rawaya mai cin Darɓa. Ita ma tana taimaka ma wake. Ana iya amfani da su dan kashe Darɓa in ba bu maganin ƙwarin wake.

**Français** – Coccinelle
**Hausa**-Mai shayi ukku rawaya
**Scientifique** – *Cheilomenes vicina*

## Kaska Kwafsar Wake



**Hausa** – ƙarbobo
**Français** – Punaise brune
**Scientifique** – *Clavigralla tomentosicollis*



**Hausa** - yaya
**Français** –jeunes punaises brunes
**Scientifique** – *Clavigralla Tomentosicollis*

Wannan ƙwarin masu suna ƙarbobo suna rayuwa kwana 24 zuwa kwana 84. Ƙarbobo yana iya kashe wake cikin kwafsarshi saboda yana shan ruwan wake daga tsanwa kwafsar. Ana iya kashe ƙarbobo da maganin zamani ko na gargajiya.



**Hausa** – baƙi karbobo
**Français**– Punaise noire
**Scientifique** – *Anoplocnemis curvipes*



**Hausa** – yayan baƙin karbobo
**Français** – Larves punaise noire
**Scientifique** – *Anoplocnemis curvipes*

Wanan ƙwaron mai suna baƙin karbobo yana rayuwa kwana 24 zuwa kwana 84. Yana barna kamar kowane karabobo. Ɗiyan shi suna taruwa ƙasan kunnan wake kuma suna kama da tururuwa. Ana iya kashe shi da maginin zamani ko na galgajiya.

## Kaska Hure da Kwafsar Wake



**Hausa** - Malam Batata
**Français** - Maruca

Malam Batata ne ke bada wanan tsutsar da ke cin hure da Kwafsa. Yana rayuwa kwana 7 kuma yana sakin har ƙwai 150 bisa hure da Kwafsar wake.



**Hausa- Tsutsar Malam Batata**
**Français**– Larve Maruca



**Hausa - tsutsar Malam Batata**
**Français** – Larve Maruca

Ana iya kashe Malam Batata da maginin zamani ko na gargajiya.

**N° 007-2013/INRAN**